# Fa’idojin Mayar da Harshe zuwa Fasahar Zamani

TRANSLATION COMMONS

2022-2032 | INTERNATIONAL DECADE OF
Indigenous Languages

# Fa'idojin Mayar da Harshe zuwa Fasahar Zamani

Muna fatan cewa zango-zangon jagororin Daga Sifili zuwa Fasahar Zamani za su samar da bayyananniyar hanya ga kowace al'ummar harshe da ke da sha'awar mayar da harshenta zuwa fasahar zamani idan tana burin cin gajiyar cikakken ikon amfani da kwamfuta a harshenta na asali.

Fa'idojin mayar da harshe zuwa tsarin fasahar zamani zai dogara ne kan manufofin al'ummar da ke magana da shi. Hakan na iya haɗawa da karrama kyawun harshen, kiyaye tsarin ilimi, yaɗa kyawawan ɗabi'u, ƙirƙirar manhajoji da kayayyaki, yaɗa labarai da tarihi, sauƙaƙa kula da muhalli da jagoranci a fannin tunani, da kuma faɗaɗa kasuwanci, ilimi, samar da ayyukan yi, nishaɗi, lafiya da kuma tsaro. Mayar da harshe zuwa fasahar zamani yana ba al'umma damar cin gajiyar tarin kayan aikin kwamfuta na ci gaba don kiyayewa, farfaɗowa da kuma koyar da harshe. Kasancewar harshen a intanet, wanda hakan zai ƙara fito da martabarsa, na iya taimakawa wajen yin tasiri ga manufofin gwamnati don tallafa wa al'ummomin asali da kuma jawo hankalin kamfanoni zuwa ga samar da daidaito. Ganin yadda matasa suka mamaye amfani da wayoyin zamani, mayar da harshe zuwa fasahar zamani na iya zama wata sahihiyar hanyar jawo hankalinsu ga harshensu na asali. Samun damar bayyana harshe a fannonin fasahar zamani na iya haifar da ƙarin dama da kuma buƙatar ƙwararrun masu jin harshen asali.

Yayin da al'ummomin harshe suka mamaye duniya ta hanyar fasahar zamani, hakan yana amfanar duniya baki ɗaya. Gogewa, ilimi, da ra'ayoyinsu na musamman za su zama wata gagarumar gudummawa ga sauran sassan duniya, sannan sakamakon haɗin gwiwar zai iya kawo sabbin hanyoyin magance matsalolin duniya. Mayar da harshe zuwa fasahar zamani yana sauƙaƙa taskancewa da kuma wallafa waɗannan bayanan, wanda hakan zai sanya yalwar asalin harshen ɗan-adam ta wanzu a duniya, kuma a adana shi don amfanin ɗan-adam ta hanyoyin da ba za mu iya hasaso su ba a yanzu.

A taƙaice, wasu daga cikin fa'idojin da ake samu ta hanyar mayar da harshe zuwa fasahar zamani su ne:

- Ba masu jin harshe guda damar samun bayanai, ƙirƙira, da musayar abubuwan da ke cikin harshen asali cikin sauƙi, har ma da nesa, ga daidaikun mutane ko kuma mutane da yawa.
- Ƙara damar samun bayanan likitanci da na kiwon lafiya.
- Tallafa wa hanyoyin sadarwar gaggawa da na annoba don ceton rayuka.
- Faɗaɗa kasuwancin gida da na intanet.
- Samar da sabbin hanyoyin yaɗa fasaha, jagoranci a fannin tunani da kuma falsafa.
- Samar da kayan koyarwa na harshen asali.
- Kyautata alaƙa da sadarwa da maƙwabta.
- Kyautata hanyoyin sasanta rikici.
- Ba da damar fafutuka da samun hanyoyin shari'a da na gudanar da mulki a harshen asali.
- Ƙara damar samun bayanai a Intanet don ilimi, kasuwanci, da ba da gudummawa, walau a harshen asali ko wasu harsunan yayin da kayan aikin fassara ke bunƙasa.
- Sanya wasu su fahimci harshen asali, al'adu da hikimomi.
- Faɗaɗa matsayi da fito da martabar al'ummomin asali a faɗin duniya.
- Ba wa mutanen da aka mayar baya ko tsirarun harsuna damar ɗorewa ko farfaɗo da harshensu ko da manyan al'ummomi sun mamaye su.
- Taskance tsarin ilimin asali, al'adu, tarihi, fasaha, magani, hikima, kyawawan ɗabi'u, da kuma ra'ayoyin duniya.